# Matsayina da duniya, ni a cikinta ba komai bane sai kamar matafiyi ne akan abin hawa da ya sha inuwa a ƙarƙashin wata bishiya sannan ya tafi ya barta

Daga Abdullahi ɗan Mas'ud - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya yi bacci akan wata tabarma, sai ya tashi haƙiƙa ta yi masa tabo a gefensa, sai muka ce: Ya manzon Allah, inama dai a ce mun yi shimfiɗa saboda kai, sai ya ce: "Matsayina da duniya, ni a cikinta ba komai bane sai kamar matafiyi ne akan abin hawa da ya sha inuwa a ƙarƙashin wata bishiya sannan ya tafi ya barta".

[Ingantacce ne] [Tirmizi ne ya Rawaito shi]

Abdullahi ɗan Mas'ud - Allah Ya yarda da shi - ya ambaci cewa annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya yi bacci akan shimfiɗa ƙarama wacce aka saƙata da wasu daga tsirrai, sai ya miƙe alhali tabarmar ta yi tabo a fatar gefensa, sai muka ce: Ya manzon Allah, ina ma dai a ce mu yi maka wata shimfiɗa mai laushi da hakan ya fi kyau daga kwanciyarka akan wannan tabarmar mai kaushi, sai (annabi) tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya ce: Ni bana son sabo da duniya har in yi kwaɗayi a cikinta, kwatankwacina da wanzuwa a cikin duniya bai zama ba sai kamar wani matafiyi ne da ya sha inuwa ƙarƙashin wata bishiya sannan ya tafi ya barta.



النجاة الخيرية
ALNAJAT CHARITY
لجنة الدعوة الإلكترونية
EDC E-Da'wah Committee